# 3 Yahaya

1 Daga dattijon zuwa ga Gayus, wanda nake
kauna da gaske.
2 Ya kaunatace na, ina addu'a domin ka samu
albarka cikin kowanne al'amari, da kuma koshin
lafiya, kamar yadda ruhun ka yake lafiya.
3 Na yi farin ciki kwarai sa'adda wadansu
'yan'uwa suka zo suka ba da shaida a kan
bangaskiyar ka, kamar yadda ka ke bin gaskiya.
4 Ba abin da ya fi faranta mani rai kamar in ji
yayana suna tafiya cikin gaskiya.
5 Ya kaunatace na, kana aiki da aminci zuwa
ga 'yan'uwa da baki,
6 wadanda suka shaida kaunar ka a gaban
ikilisiya. Zai yi kyau ka yi masu taimako da
kyakkyawar salama, ta hanyar da ta dace da
masu ibada,
7 domin sabili da sunan nan ne suka fito, ba su
kuma karbar kome a hannun al'ummai.
8 Don haka ya kamata mu karbi irin wadannan
mutane, domin mu zama abokan aiki tare da su
a kan gaskiya.
9 Na rubuta wasika zuwa ga ikilisiya, amma
Diyotariffis, wanda ya fi kowa son girma a
cikinsu, bai karbe mu ba.
10 Saboda haka, idan na zo, zan tuna masa
da irin ayukkan sa, da kuma yadda yake bab-
bata sunayen mu a wurin jama'a da miyagun
kalmomi. Wannan ma bai ishe shi ba, har
ma yana kin karbar 'yan'uwa. Ya kuma hana

wadanda suke son su yin hakan, harma ya kan
kore su daga ikilisiya.
11 Ya kaunatace na, kada ka yi koyi da mugun
abu, sai dai abu mai kyau. Dukan wanda
yake yin abu mai kyau na Allah ne; mai aikata
mugunta kuma bai san Allah ba.
12 Dimitiriyas yana da kyakkyawar shaida a
gun kowa har a wurin gaskiyar da kanta. Mu ma
mun shaida shi, ka kuma san shaidar mu gaskiya
ce.
13 Ina da abubuwa dayawa da zan rubuta
maka, amma ban so in rubuta maka su da
alkalami da tawada ba.
14 Ina sa zuciya mu sadu ba da dadewa ba,
sa'annan mu yi magana ido da ido.
15 Bari salama ta kasance tare da kai.
Abokanmu suna gaishe ka, kuma ka isadda
sakon gaisuwar mu ga sauran abokai da sunayen
su.

# Litafi Mai-tsarki

## The New Testament in the Hausa language of Nigeria

copyright © 2020 Door43 World Missions Community

Language: Hausa

Translation by: Alakirawa, Bayan, Chrispher Ishaya, Dabere, Dacuhus Timothy Danjuma, Danjay, Danjuma Alfred H, Euang Hediza Naohammed, Franklyn Ukazu Udochukwu, Gideon, Gokop, Habibu, James, Kiash Dachung Butus, Lazarus, Nadaki M. Philip, Nenching, Paul, Rebecca, Rev. Ayuba Taiba, Rev. Cain Yusuf Daniel, Rev. Dalhatu Dambo Ayuba, Rev. Dr. Tambanya Yahaya, Rev. Dr. Yakubu Hassan, Rev. Hannatu Samuel Ndberhukwu, Rev. Ibrahim Kassim, Rev. M. Dan'Amarya, Rev. Yakuba Ayuba

Contributor: Dacuhus Timothy Danjuma, Euang Hediza Naohammed, Kiash Dachung Butus, Nadaki M. Philip, Rev. Ayuba Taiba, Rev. Cain Yusuf Daniel, Rev. Dalhatu Dambo Ayuba, Rev. Dr. Tambanya Yahaya, Rev. Dr. Yakubu Hassan, Rev. Hannatu Samuel Ndberhukwu, Rev. Ibrahim Kassim, Rev. M. Dan'Amarya, Rev. Yakuba Ayuba

This translation is made available to you under the terms of the Creative Commons Attribution Share-Alike license 4.0.

You have permission to share and redistribute this Bible translation in any format and to make reasonable revisions and adaptations of this translation, provided that:

- You include the above copyright and source information.
- If you make any changes to the text, you must indicate that you did so in a way that makes it clear that the original licensor is not necessarily endorsing your changes.
- If you redistribute this text, you must distribute your contributions under the same license as the original.

Pictures included with Scriptures and other documents on this site are licensed just for use with those Scriptures and documents. For other uses, please contact the respective copyright owners.

Note that in addition to the rules above, revising and adapting God's Word involves a great responsibility to be true to God's Word. See Revelation 22:18-19.

2020-06-19

---

PDF generated using Haiola and XeLaTeX on 18 Apr 2025 from source files dated 31 Aug 2023

31fd93a8-6c61-5e08-ad99-3312611b0f4b